**JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA** **18 Jimada al- Ah-khir, 1443**

**MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI** **21 Junairu, 2022**

(1)

**TOBULAN GINA IYALI DA HANYOYIN BA SU KARIYA**

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(A cikin ayoyinsa ne –mai girma da ɗaukaka- ya halitta maku abokan zamanku daga cikinku, saboda ku sami sukuni da** natsuwa **a wurinsu, ya kuma sanya soyayya da tausayi a tsakaninku, lallai a cikin wannan abu akwai ayoyi masu yawa ga mutanen da suke tunani)** [ar- Rum: 21], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai samun tsarin iyali a cikin rayuwar ɗan Adam ɗaya ne daga cikin manyan ni'imonin Allah mai girma buwaya, lallai Allah ya bayyana wa bayinsa wannan ni'ima a cikin littafinsa mai girma, a inda mai girma da ɗaukaka yake cewa: **(Allah ya halitta maku abokan zama na aure daga cikin jinsinku saboda ku sami natsuwa a tare da su, ya kuma halatta maku 'ya'ya da jikoki daga abokan zaman naku na aure, ya kuma azurta ku da abubuwan da suke faranta rai. Yanzu duk wa waɗannan abubuwa ne kuma wasu mutane suke haɗa shi da wasu a wurin bauta? Su yi imani da ɓata, su yi wa ni'imar Allah da ake gani ƙiri- ƙiri butulci, wadda ta cancanci su yi godiya akan, su kuma tsarkake yin bauta ga Allah shi kaɗai)** [an- Nahli: 72].

Iyali iri ne na samuwar al'umma, kuma nan ne sansani na farko na bai wa al'umma kariya; saboda haka ne addinin

Musulunci ya muhimmanta gina iyali akan turba mai ƙarfi da inganci, ta yanda zai zama a haɗe, abin da zai tabbatat da samuwar soyayya, da tausayi tsakanin waɗanda suke ciki; ta yanda aminci, da kwanciyar hankali za su karaɗe dukan al'umma a rayuwarsu ta zamantakewa, saboda haka ne shari'ar Musulunci ta zo da wajibcin yin taka- tsatsan wajen zaɓan abokin zama na aure, wanda irin wannan zaɓin zai haifar da kwanciyar hankali a rayuwar aure, haka ma Shari'ar Musulunci ta faɗakar akan muhimmancin ɗaukan alhaki ta dukan fagage na ɗawainiyar kuɗi, da na zamantakewa, da ma na mutuntaka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ya ku taron matasa, duk wanda yake da ikon yin aure to ya yi aure, saboda shi ne abin da ya fi taimakawa wajen hana gane- gane, da kuma kiyaye yin alfasha, wanda kuma ba shi da daman yin aure, to ya kame, wannan ma magani ne a gare shi).**

Haka ma Shari'ar Musulunci ta bayar da kulawa ta musamman wajen tarbiyyantar 'ya'ya akan kyakkyawar turba, da ɗaura su akan alhakin da yake akansu na addini, da na zamantakewa, da na ƙasa, abin da hakan zai kai zuwa ga gina tsarin iyali nai ƙarfi da nagarta, ta hanyar dasa kyawawan ɗabiu na addini, da na zamantakewa, da al'adu masu nagarta a cikin zukatan 'ya'ya, lallai 'ya'ya amana ne a wuyan iyayensu, Allah mai girma yana cewa: **(Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku katange kawunanku da iyalanku ga barin wutar da mutane da duwatsu su ne makamashinta)** [at- Tahrim: 6], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah zai tambayi kowane mai kulawa akan abin da ya ba shi kulawa da shi, shin ya kula da shi ne, ko ya tozartar da shi? Kai har sai an tambayi mutum akan iyalan gidansa)**, haka ma idan 'ya'ya

suka zama nagartattu hakan wani abu ne na jin daɗi, da kwanciyar hankali ga iyaye maza da mata a duniya da lahira, Allah Maɗaukain Sarki yana cewa: **(Su ne waɗanda suke cewa: Ya Ubangijinmu ka ba mu abokan zama na aure da zuriya da za su zama jin daɗi da kwanciyar hankali a gare mu, ka sanya mu zama jagororin masu tsoron Allah)** [al- Furƙan: 74], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Idan ɗan Adam ya rasu dukan ayyukansa za su tsaya in banda guda uku: sadaka mai gudana, ko ilimin da ake amfana da shi, ko ɗa na gari da yake yi masa addu'a).**

Lallai Annabinmu mai yawan karamci (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya bayyana mana cewa mutumin da ya fi kowa zama alhairi a cikin maza da mata, shi ne: wanda ya fi kyautata wa iyalansa, (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Wanda ya fi alhairi a cikinku shi ne wanda ya fi zama alhairi ga iyalansa),** lallai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) shi ne ya fi zama alhairi ga iyalansa, madalla da shi a matsayinsa na miji, madalla da shi a matsayinsa na uba, madalla da shi a matsayinsa na kaka, duk mutumin da bai zama alhairi ga iyalansa ba, to da ma can babu wani alhairi a tare da shi.

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai Musulunci yana bayar da dukan kulawa wajen kiyaye tsarin iyalai, ta yanda za su zama a haɗe cikin soyayya, da mutunci, gami da girmama juna a tsakaninsu, duk wanda yake bibiyar Alƙur'ani mai girma zai ga irin yanda ya girmama mace,

ya sanya ta zama abokiyar zama ga namiji, shi ya sanya a cikin Alƙur'ani mai girma babu kalmar "Zaujatu" da ma'anar mata, kaman dai Alƙur'ani mai girma ya ɗauki lafuzzan da suke nuni zuwa ga daidaito ne wajen bayyana jinsi biyu, kai har ma da wurin ishara na ma'ana, Allah mai girma yana cewa: **(Su ɗin sutura ne a gare ku, ku ma sutura ne a gare su)** [al- Baƙra: 187], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Suna da haƙƙoƙi daidai da wajiban da suke akansu cikin kyautatawa)** [al- Baƙra: 228], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Maza suna da rabo a cikin abubuwan da suka aikata, su ma mata suna da rabo a cikin abubuwan da suka aikata)** [an- Nisa'i: 32], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) a gamammiyar huɗubarsa ta Hajjatul wada'i yana cewa: **(Ku sani cewa kuna da haƙƙi akan matanku, su ma matanku suna da haƙƙi akanku).**

Ita rayuwar ma'aurata biyu ta ginu ne akan natsuwa, da soyayya, da tausayi, da kuma haƙƙoƙi da wajibai a tsakaninsu, babu wani batu na rinjaye, ko neman yin nasara akan juna, ko kuma nuna iko, ba zai taɓa yiwuwa rayuwar aure ta ginu akan rinjaye, da yin galaba, ko nuna iko ba, a'a tana ginuwa ne a yanayi na girmama juna, da ganin mutuncin juna, kuma dukan ɓangarorin mata da mijin su cigaba da aiki wajen sana'anta farin ciki, da kuma haƙuri da juriya akan dukan wahalhalu da fuskantar ƙalubale, Sayyiduna Abuddarda'i (Allah ya ƙara yarda da shi) yakan ce wa matarsa: Idan kin ga na yi fushi, ki lallashe ni, ni ma idan na ga kin yi fushi zan lallashe ki, in ba haka ba, ba za mu iya zama da juna ba.

Lallai babu abu mafi kyau da ya kai iyalai su rayu a cikin yanayin mai cike da natsuwa, da kwanciyar hankali, ta yanda za su samar da jin daɗin duniya da na lahira.

**Ya Ubangijinmu ka ba mu abokan zama na aure da zuriya da za su zama jin daɗi da kwanciyar hankali a gare mu, ka sanya mu zama jagororin masu tsoron Allah.**